# LESSON 27: KARATUN GAJERUN LABARAI - READING SHORT STORIES

Ado yaro ne mai ƙwazo. Duk aikin da aka saka shi yana iya bakin ƙoƙarinsa ya ga cewa ya aiwatar da aikin daidai. Ƙari a kan haka kuma yana da nagarta, domin ba kasafai ake samun ha'inci a cikin aikinsa ba. Saboda haka idan har ka ga an saka Ado aiki bai yi ba, to haƙiƙa wannan aikin ya fi ƙarfinsa.

Ka san halin yara akwai su da wasanni, amma duk da haka Ado akwai mayar da hankali. Ko ka taɓa lura da cewa kullum shi yake fara zuwa makaranta? Kuma idan ka lura Ado bashi da abokin faɗa tun da ya shigo makarantar nan. Ni na lura sosai ko hutun rabin lokaci aka fito idan har bashi da kuɗin kashewa yakan zauna a aji ya yi ta karanta littattafansa har lokacin ya ƙare a koma a taras da shi a aji. Wannan kuwa halayya ce mai kyau wadda ke nuna rashin kwaɗayinsa da kuma rashin damuwa da kayan wani. Kai! Amma fa ina yi wa wannan yaro fatan alheri a rayuwa.